**EPISODE 23**

Characters

*Laraba*

*Inna*

*Hannah*

*Danjuma*

*Tina*

*Asabe*

**Scene 1**

*Community Clinic. Morning*

| | | |
|---|---|---|
| **1.** | **SFX:** | **MURMURING SOUND OF CLINIC WAITING ROOM AMBIENCE WITH PATIENTS MURMURING AND A BABY CRYING** |
| **2.** | **SFX:** | **RAPID FOOTSTEPS APPROACHING** |
| **3.** | **LARABA:** | **(SLIGHTLY OUT OF BREATH)** Ah ina kwana Nas Hajara. Na *d*an yi latti yau fa. Yi hakuri, sai da naje na raka Mamata tasha. Bari na *d*auki wa*d*annan katunan marasa lafiya … |
| **4.** | **ASABE:** | **(COMING ON, INTERRUPTS, SHOUTING)** Laraba! **(PAUSES, THEN SHOUTS AGAIN)** Eh! Nice nake kiran ki Laraba! |
| **5.** | **LARABA:** | **(CONFUSED)** Asabe? |
| **6.** | **ASABE:** | O-ho kina mamakin da kika gan ni tare da rai da lafiya ko, Laraba?! |
| **7.** | **LARABA:** | **(CONFUSED)** Maganar menene kike yi Asabe? Me yasa kika kawo mini hayaniya wajen aiki na? |
| **8.** | **ASABE:** | Oho! Kina son ki nuna kamar baki san komai ba ko, Nas Laraba?! Kina tsammani ban san sirrinki bane? Allah Ya tona asirinki Ya kare mun iyali na daga sharrinki! Mayya kawai! |

| | | |
|---|---|---|
| **9.** | **LARABA:** | **(BECOMING UPSET)** Asabe, idan baki da abun fa*d*i ki je gida kawai! |
| **10.** | **ASABE:** | **(LOUDLY)** Eh-eh-eh, kar ki ta*b*a ni da la'antaccen hannayenki! |
| **11.** | **LARABA:** | Asabe, ki rage muryar ki don Allah! Wannan asibiti ne ba kasuwa bane. |
| **12.** | **ASABE:** | **(LOUDLY)** Oh kina gaya mun nayi shiru ko? Ba zan yi shiru ba fa Laraba! Ba zaki iya hana ni magana ba. |
| **13.** | **LARABA:** | **(UPSET)** Asabe, don Allah ki natsu. |
| **14.** | **ASABE:** | **(SHOUTING)** Hmmm mutane! Ina fata kuna ji. Wannan Nas Laraba na da rashin sa'a daga garinsu! |
| **15.** | **LARABA:** | **(ANGRY)** Asabe! Ki fita! |
| **16.** | **ASABE:** | **(SHOUTING)** Hmmm in kuna so ku bar Nas Laraba ta ta*b*a ku fa. Duk wanda ya kusance ta sai ya samu da mumunar mutuwa! |
| **17.** | **SFX:** | **<u>SOUNDS OF COLLECTIVE GASPS</u>** |
| **18.** | **LARABA:** | Wato Asabe, yanzu da kika fa*d*i abun da kike son ki fa*d*a, kin ji da*d*i ko? |
| **19.** | **ASABE:** | **(RUDELY)** Hmmm Laraba, yanzu na fara dake. Ban ma je da nisa ba kenan. |
| **20.** | **LARABA:** | Asabe don Allah ki je gida kawai! |
| **21.** | **ASABE:** | Yana da kyau Laraba, yana da kyau da kika kira gida na. sai kin fita fa! Ba zan iya zama tare dake a cikin gidan! |
| **22.** | **LARABA:** | Hmmm Asabe, Hajiya Inna ce kawai zata iya yanke wannan shawara, idan bata gaya mun haka ba, babu wani fita da zan yi! |
| **23.** | **ASABE:** | Banzan mata kawai, me yasa baki gidan miji eh? Me yasa baza ki je can inda ya dace miki ba? Maganar banza! |
| 24. | **LARABA:** | **(ANGRILY)** Toh Asabe, na ji! Abun da kike so kenan? Kin samu biyan bu*k*ata! Zan tafi! |
| 25. | **MUSIC:** | **<u>BRIDGE MUSIC</u>** |

**Scene 2**

*Danjuma and Hannah's Residence.*

**26. SFX:** **SOUND OF A KNOCK ON A WOODEN DOOR**

**27. TINA:** Na'am? Wanene?

**28. SFX:** **SOUND OF DOOR BEING OPENED**

**29. HANNAH:** **(SHOCKED)** Tina! Har yanzu kina nan? Zama tare da Danjuma?

**30. TINA:** **(RUDELY)** Oh Hannah, ke ce. Ina kuma zan zauna in ba tare da masoyi na ba Danjuma?

**31. HANNAH:** **(ANGRY)** Kalli nan Tina, bani da lokacin ki. Ina Danjuma yake?

**32. TINA:** Bai dawo daga aiki ba.

**33. HANNAH:** Tina, baki jin kunya? Me yasa  kike nan har yanzu eh?

**34. TINA:** Ni ya kamata nayi miki wannan tambayar.

**35. HANNAH:** Ehn? Gwara ki tattara kayayyakinki ki bar mini gida na yanzu-yanzu!

**36. TINA:** Ina da hakkin zama a wannan gida kamar yadda kema kike dashi.

**37. HANNAH:** Kina hauka ne Tina, eh?

**38. TINA:** Bari ya huce ke kawo rabon wani! Danjuma na so na matu*k*a, bari na gaya miki!

**39. HANNAH:** Kalle ta! Wannan Danjuman dai dake zuwa zaure na kullun yana ro*k*o na dawo.

**40. TINA:** Ahap!

**41. HANNAH:** Kar ki manta cewa ni matarsa ce, kuma uwar yaronsa, ke ba komai bace!

**42. TINA:** 'Yar uwa, in baki da labari, Danjuma ya neme ni da aure, saboda haka duk wannan da kike yi ….

**43. HANNAH:** **(CUTS IN, SHOCKED)** Me?! Tina me kika ce??

**44. TINA:** **(LAUGHS MOCKINGLY)** Hannah, kin zama tsohon yayi 'yar uwa. Da kina da kuzarin da nake dashi da kin *d*an samu dama.

45. **HANNAH:** Kai! Baki da godiya Tina! Ina bakin cikin kawo ki cikin gida na!

46. **TINA:** **(LAUGHS MOCKING)** Tafi can Hannah. Kin bar mun *d*akin auren ki, ko ba haka ba? Danjuma ya zama nawa yanzu!

47. **SFX:** **DOOR SLAMS SHUT**

48. **MUSIC:** **BRIDGE MUSIC**

**Scene 3**

*Hajiya Inna's Residence. Evening.*

49. **SFX:** **SOUND OF KNOCK ON DOOR FOLLOWED BY DOOR BEING OPENED**

50. **INNA:** Laraba, Salam alaikum.

51. **LARABA:** Waalaikum salam, Hajiya Inna.

52. **INNA:** Laraba, me yasa da*k*inki na harzi*k*e?

53. **LARABA:** Ina kwashe kaya na Inna!

54. **INNA:** Kwashe kaya? Me yasa? Ina zaki je Laraba?

55. **LARABA:** Hajiya, zan bar wannan gidan da yamman nan.

56. **INNA:** Laraba, menene nayi miki har kika yanke wannan *d*anyar shawarar?

57. **LARABA:** Inna ba ke bace.

58. **INNA:** Don Allah kar ki fita haka kawai! Ki gaya mun dalilin da yasa kike son ki fita.

59. **LARABA:** Inna… **(PAUSES)** bari na gyara miki waje ki zauna. Kiyi ha*k*uri.

60. **SFX:** **BED CREAKS AS INNA SITS ON IT**

61. **INNA:** Toh Laraba, ki gaya mun. me yasa kika yanke shawarar fita?

62. **LARABA:** Hajiya, yau da safe Asabe ta zo wajen aiki na a asibiti ta jawo hayaniya, tana zagi na cewa sai na fita daga gidan nan.

63. **INNA:** Ai na san sai da hannun wannan yarinyar a cikin maganar.

64. **LARABA:** Ta kunyatad dani sosai Inna, tana bayyana sirri na a cikin jama'ar asibiti, tana cewa na dauki rashin sa'a na in fita daga wannan gidan.

65. **INNA:** Ha! Wace irin abu ne kuma wannan?

66. **LARABA:** Kin ga Hajiya Inna, ina ta hakuri da Asabe domin ni 'yar zaman gidan haya ce. Amma domin zaman lafiya, ni zan yi tafiyata kawai!

67. **INNA:** A'a! zamu sasanta wannan abun tun yanzu! **(SHOUTING)** Asabe! **(PAUSE)** ASABE!!

68. **ASABE:** **(SHOUTING FROM OFF-MIC)** *Na'am* (yes) Inna. Ina zuwa!

69. **SFX:** <u>**SOUND OF HURRIED FOOTSTEPS APPROACHING THE ROOM**</u>

70. **ASABE:** **(COMING ON, SLIGHTLY OUT OF BREATH)** Na'am Hajiya Inna, kin kira ni?

71. **INNA:** Asabe, ban san lokacin da zaki fara *d*aukar girmanki eh! Me kika gaya wa Laraba? Eh?

72. **ASABE:** Inna, na ji ki tare da Hajiya Lantana kuna magana akan tarihin Laraba, sai nace ya kamata na kare mana iyalenmu …

73. **INNA:** **(INTERRUPTS)** Kin ji mu ko kuma kin la*b*e kina sauraren mu? **(SUCKS TEETH)**

74. **ASABE:** Erm Hajiya…

75. **INNA:** **(SUCKS TEETH)** Ki cigaba! Kar ki girma ko! Ki cigaba da yin shirme a cikin jama'a, kin ji ko?

76. **LARABA:** **(HESITANTLY)** Inna ina ganin tana da gaskiya da ta ce ina da rashin sa'a.

77. **INNA:** Ki yi mun shiru a wajen nan! Babu me rashin sa'a! Toh bari na gaya miki wani abu: maciji ya harbi mijina na farko a daren da muka yi aure.

78. **LARABA:** **(SHOCKED)** Da gaske?

79. **INNA:** Eh, an camfe ni da rashin sa'a sai na fita daga *k*auyen mu a Borno na dawo Kaduna inda na ha*d*u da Baban Hassan na aure shi.

80. **LARABA:** Lalle! Inna!

81. **ASABE:** Inna ban sani ba fa!

82. **INNA:** Ke kuma Asabe, mamanki bata mutu wajen haihuwarki ba? Kuma ba babanki ya mutu da zazza*b*in cizon sauro kafin kika cika shekara *d*aya ba?

83. **ASABE:** **(HUMBLY)** Eh Hajiya, haka ne.

84. **LARABA:** Da gaske?

85. **INNA:** Kuma baki gani Laraba, tana zaman lafiya tare da mijinta da yaransu? Tsautsayi na iya fa*d*uwa akan kowa. Kar ki yarda wani ya gaya miki wai ke kika jawo rashin sa'ansu.

86. **ASABE:** Hajiya nagode da kika maido ni kan hanya, nayi kuskure Laraba. Kiyi hakuri da duk abun da nayi miki, ki yafe mun.

**Scene 4**

*Danjuma's Residence.*

87. **SFX:** **<u>SOUND OF KEY OPENING A DOOR FOLLOWED BY DOOR OPENING</u>**

88. **SFX:** **<u>SOUND OF TV IN BACKGROUND</u>**

89. **TINA:** Ah Danjuma! Ka dawo?

90. **DANJUMA:** Tina, me kike yi a nan?

91. **TINA:** **(LAUGHS)** Oh na zo ne nayi maka wasu aikace-aikace ne sai lokaci ya *k*ure mun.

92. **DANJUMA:** Kalli nan Tina, na gaya miki bai dace ki zo nan ba. Bana jin da*d*in zuwanki nan, musamman da nake ni ka*d*ai a nan.

93. **TINA:** **(FLIRTATIOUSLY)** Ah amma Danjuma, saboda kai ka*d*ai ne shi yasa nake zuwa na share gidan, na kuma dafa maka abinci.

94. **DANJUMA:** **(IMPATIENTLY)** Na riga na gaya miki cewa ba sai anyi haka ba Tina.

95. **TINA:** Toh, cewa nayi tunda Hannah ta *k*i ta dawo gida, kuma ma ba zata yi maka magana ba, bai kamata nima nayi rashin hankalinta ba.

96. **DANJUMA:** **(UPSET)** Ban san me yasa zata zarge ni kamar haka ba!

97. **TINA:** Hmm *k*ila tana neman a kula ta ne kawai! Hm! Yanzu zaka cigaba da bin Hannah? Koda yake, abun da take so kenan. Ta cika ji kamar ita wata zinariya ce **(SUCKS TEETH)**

98. **DANJUMA:** Kar kiyi maganar Hannah haka. *K*ila ba zan gane abun dake faruwa ba amma matata ce, kuma ba zan huta ba sai na dawo da ita.

99. **TINA:** Hm! Toh fa Danjuma, amma bari na saka maka abinci ko?

100. **DANJUMA:** Tina, ba zan iya cin wani abu yanzu ba! Sai na je na ga Hannah.

101. **TINA:** **(IRRITATED)** Hmmm Danjuma, haba! Ba zaka ko ta*b*a wani *d*an abu ba?

102. **DANJUMA:** Kalli nan Tina, nagode da duk abun da kika yi domin taimaka mini a wannan lokacin da nake da bu*k*ata, amma ina ganin ya kamata ki daina zuwa nan.

103. **TINA:** **(UPSET)** Amma ba komai bane ai!

104. **DANJUMA:** Na sani, amma don Allah ki bani makullinki na gidan Tina.

105. **TINA:** Ha! Danjuma! Wannan ba lalle bane ba ai!

106. **DANJUMA:** Kalli nan Tina, ina miki godiya amma bana son ki sake zuwa nan kuma, don Allah. Bai dace ba da matata bata nan.

107. **MUSIC:** **<u>BRIDGE MUSIC</u>**